**KOMAI NISAN JIFA III**

**EPISODE 2**

**Characters**

*Hannah*

*Danjuma*

*Hassan*

*Husseini*

*Kande*

*Laraba*

*Lantana*

**EPISODE 2, SCENE 1**

**Southern Kaduna. Hannah and Danjuma's Residence. Late Afternoon.**

| | | |
|---|---|---|
| **1.** | **MUSIC:** | **THEME MUSIC UP AND UNDER…** |
| **2.** | **SFX:** | **KEY TURNS IN LOCK AND DOOR OPENS AND CLOSES OFF MIC. FEMALE FOOTSTEPS COMING ON MIC AS…** |
| **3.** | **DANJUMA:** | **(ON MIC)** Aah, masoyiyata Hannah – kin dawo. |
| **4.** | **HANNAH:** | **(WEARILY ON MIC)** E, masoyi na (**SIGHS, BROKEN)** Hmm Danjuma, na sha wuya fa. |
| 5. | **DANJUMA:** | Don Allah kada ki yi kuka, Hannah… **(SOFTLY)** ya ki taho….. |
| 6. | **HANNAH:** | **(TEARFUL)** na sha kuka wannan makon, bana tsammanini ina da raguwar hawaye, Allah sarki Laraba. |

7. **DANJUMA:** **(SYMPATHETIC)** gaskiya abin takaice ne, wannan irin bala'i! Amma ba komai abin kauna ta, kada ki yi kuka….

8. **HANNAH:** **(SNIFFLING)** Oh Ya Allah… Laraba ta ga tashinhankali iri iri tun tana yar yarinya, ya mata yawa….

9. **DANJUMA:** Yayi yawa ma koma wanene ai, bakin jinni ne kawai….

10. **HANNAH:** **(HEATED)** Kada kayi magana haka! Har da kai Danjuma! Kul! Kada ka sake fadar haka.

11. **DANJUMA:** **(SURPRISED)** Ah ah Hannah, me na fada na bacin rai?

12. **HANNAH:** **(UPSET)** Bakin Jini…. Don Allah kada ka zama ka mar mugayen yan garin su Laraba mana, da suka yi mata lakani da mai bakin jinni.

13. **DANJUMA:** Haba, Hannah, ne ban taba ce mata mai bakin jinni ba ai!

14. **HANNAH:** Ka kira ta mai bakin jinni mana.

15. **DANJUMA:** Aah. Ni abin da nace ai abin da ya faru abin bakin jinni ne, rashin wanda mutum ke mutukar so a ranar bukin ai bala'i ne, kyakyawar misalin bala'i.

16. **HANNAH:** **(INTERRUPTS)** Yauwa! Ka sake fada ai!

17. **DANJUMA:** haba! Hannah, baki kyautawa fa, ki bari in gama magana mana, ban ce ita ke da bakin jinni ba ai.

18. **HANNAH:** Danjuma, kayi hakuri, raina ne ke baci da abinda jama'a ke fade da yi ma Laraba

19. **DANJUMA:** Me jama'a ke fade game da ita?

20. **HANNAH:** Sun dauko bala'in hadarin gobaran da ta hanlaka iyayenta da yan'uwanta na sama da shekaru 20 sun hada da rasuwar wanda zata aura, kuma ana yi kamar wata aljanace ita.

21. **DANJUMA:** Kai, abin takaice, ya take fama da hakan?

22. **HANNAH:** Ba sauki a wurin ta ai, duk ida take jama'a na gunaguni akan abin, abin takaicin shine ta soma yarda da jama'ar

23. **DANJUMA:** Eyaa Laraba, ina fatan ta san muna idan tana da wane bukata …

24. **HANNAH:** **(SIGHS)** Na fada mata. Na ma ce mata ta zo mu zauna a nan, na dan lokuta, idan tana bukatar rabowa da jama'ar.

25. **DANJUMA:** Kada ki damu, abin kauna ta. Zata farfardau ba tare da dadewa ba

26. **HANNAH:** Shin….zata iya aminci da soyayyar wani kuwa

27. **DANJUMA:** e mana, zata manci ai, idan wani na garin ya taho, zai mamaye mata hankali tamkar yadda nayi miki. **(LAUGHS AND TICKLING HER)**

**28.** **HANNAH:** **(RELUCTANTLY GIGGLING)** oh oh, Danjuma, kyalei ne… daina… don allah…**(LAUGHING)** bana son inyi dariya…

29. **DANJUMA:** **(HAPPY)** Yauwa, haka yafi ai, yaki taho…**(THEY EMBRACE)** Mmmn, na ji dadin dawowar ki.

30. **HANNAH:** Ne ma haka. **(PAUSE ONE BEAT)** Danjuma, na gode,

31. **DANJUMA:** Godiyar ta mecece?

32. **HANNAH:** Da ka kyale ne na je wurin Laraba, da kuma fahintar da kayi game da alamarin

33. **DANJUMA:** **(TEASES)** Sai kin biya ne fa… ba damuwa ai,… kin ci gaba da hadiyar kwayoyin maganin tazarar haihuwan da kike chan ai, ko?

34. **HANNAH:** Hakika. **(PAUSE)** Amma, ina da bukatan mu tautauna akan tazarar haihuwar, Danju….

35. **DANJUMA:** Na'am, ina sauraron ki….

36. **HANNAH:** **(SHYLY)** Ina ganin ya chanchanta yanzu mu fara samun yaran mu, ina son in daina hadiyar kwayoyin, Me ka gani?

37. **DANJUMA:** **(SURPRISED)** Tun Yanzu? Kin tabbata?

38. **HANNAH:** E masoyi na. yanzu da na gama karatu da bautarkasa. Kawai so nake in ji ina rike da dan mu

39. **DANJUMA:** **(HAPPY)** Ni ma haka. Wai, Hannah, ina cike da farin ciki

**40. MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 2, SCENE 2**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's Resindence.**

**41. SFX:** **<u>EVENING. OUTDOORS. OUTSIDE THE COMPOUND. EVENING SOUNDS…PEOPLE PASSING ON THE STREET, A MOTORBIKE DRIVING BY…A CAR DRIVING BY FROM TIME TO TIME…</u>**

42. **HUSSEINI:** **(CLEARS THROAT. ON MIC)** Hassan, gaskiya zan fada maka, ne fa yanzu na soma gaza wa.

43. **HASSAN:** **(SYMPATHETIC)** Husseini, kada ka ce haka. Tilas ne ka cigaba da tawakali, alheri na iya nbullo wa a yan kwanakin nan.

44. **HUSSEINI:** Dan uwa, ina ma zan iya yarda da hakan

45. **HASSAN:** Toh kace min aikin kanfani bai tabbata ba kenan?

46. **HUSSEINI:** **(SADLY)** Aah

47. **HASSAN:** Ah, ah Husseini! Sun bada sanarwa cewa suna bukatan ma'aikata ai.

48. **HUSSEINI:** Gaskiya ne, amma ta nuna cewa matasa suke bukata kenan

49. **HASSAN:** **(INDIGNANT)** Maganar banza! Ina Maganar shekaru a wurin duban kwallabe? Kuma way a fada musu cewa ka tsufa?

50. **HUSSEINI:** Duk inda na je, labarin iri daya ne, ba aiki. An gaji, dubi iyalai na. idan ba dun kamna rufa min asiri ba, da yaya zanyi.

51. **HASSAN:** Haba, kar ka mayi Magana, bayan kai yan biyu na ne.

52. **HUSSEINI:** Duk da haka, na san kai ma abin ai ba kamar da ba ai, na gode da taimakon da kake yi min.

53. **HASSAN:** Ba komai, ai kai ma kana min. amma Husseini ina zancen kasuwan cin saida shayin da kake son ka fara? Kilal ka maida hankali akai kawai.

54. **HUSSEINI:** **(BITTER LAUGH)** Da me zan fara, Hassan? Hakorana? Bani da ko dari!

**55. HASSAN:** Husseini, dakata, kada mu yi watsi da dabaruntukuna. Za ka iya fara da jari ko kadan ne, ba dole sai ka fara da girma ba.

**56. HUSSEINI:** Ko da dan kalilan din bani da su, shine matsallar. Ba zan iya tambayarka domin taimako ba saboda abin da kake yi ma iyali na ai yayi yawa.

**57. HASSAN:** Husseini, kasan da ina dashi b azan yi jinkirin taimakama ba ai, amma dakata muyi nazari. Ai dole akwai mafita.

**58. HUSSEINI:** Ina maganar shago tukunna? Dole mutun yayi hayar shagon a fuskar jama'a kuma ka san irin sub a sauki ai, ina ma zan sami hayar sahgo mai sauki ba?

**59. HASSAN:** **(THINKING ALOUD)** toh Husseini, ba dole ka fara da shagon wai azo a gane ba ai, kana iya ka fara da rufar kara ma ai

**60. HUSSEINI:** E! wa zai kyalene in gina rufar kara…

**61. HASSAN:** **(INTERRUPTS, EXCLAIMING)** yauwa Alhaji Bature! Ka je ka ga Alhaji bature ka nemi taimakon sa, Yana da babbar shago a mashigar kasuwar, akwai fili da za a iya buga rufar kara a gefe Alhaji Bature!

**62. HUSSEINI:** **(CONCERNED)** Amma Hassan, kana ganin zai amince? Duk da ya san na shiga gidan yari.

63. **HASSAN:** Ba wani laifi ka gwada tambaya ai, kuma ka san Alhaji Bature yayi fiche wajen taimako

64. **HUSSEINI:** **(UNCERTAIN)** Hassan, ka tabbata? Bai ma san niba ai.

65. **HASSAN:** Husseini, baza ka sani ba sai ka gwada ai, indan ya gagara, kaje ka sami mai Unguwa zai kai ka ya gabatar da kai.

**66. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**EPISODE 2, SCENE 3**

**Southern Kaduna. Hannah and Danjuma's Residence. Afternoon.**

**67. SFX:** **DOOR BELL RINGING AND QUICK FOOTSTEPS GOES OFF MIC, TURNS KEY AND OPENS OFF MIC**

**68. HANNAH:** **(EXCITED. OFF MIC CHATTER)** Sannu da zuwa, Mama! Shigo ciki.

**69. KANDE:** **(OFF MIC)** Hannah, na gode

**70. SFX:** **FOOTSTEPS COMING ON MIC UNDER….**

**71. HANNAH:** **(UPBEAT, COMING ON MIC)** Mama, ai sai ki kira ni domin ki sanar da ni cewa kina tafei

**72. KANDE:** **(ON MIC)** ki yi hakuri, ban san cewa sai na same iz'ni zan ziyarchi ki ba.

**73. HANNAH:** Amma kin san cewa ba haka na ke nufi ba ai, da na san za ki taho da Danjuma zai aiko maki da deriba ai domin ya dauko ki.

**74. KANDE:** Ba laifi, akwai wane lokaci ai, amma ne, Kande, ban saba da hakan ba

75. **HANNAH:** Tuh, ki soma sabawa da hakan, ran Danjuma zai bace in ya same labarin cewa kina hawar motar haya domin ki ziyarce mu bayan akwai motar gida da deriba.

76. **KANDE:** Toh, shikenan Hannah, na ji, Mmmnnnh, gidan ku da da tsabta kuma da kyau, kin burge ne yata

77. **HANNAH:** Mama, na gode, amma na koya a wurin ki ne ai, bari in kawo miki abin sha.

78. **KANDE:** Ki kawo min ruwar sanyi.

79. **HANNAH:** Toh. **(GOING OFF MIC)** Kuma, na riga da na girka shinkafa wato abinicin yamma, zan kawo miki shikafar.

80. **KANDE:** Tukuna yar lailaina, na taho da brabisco da Danju harke ki so mutuka.

81. **HANNAH:** **(LAUGHING AND COMING ON MIC)** Mama, mun gode, toh ba mai cin shinkafar da na dafa kenan yau,

82. **SFX:** **<u>TRAY IS DROPPED ON TABLE AND LIQUID POURS INTO GLASS UNDER…</u>**

83. **KANDE:** Yauwa **(DRINKS, SMIRKING)** Ya Danjuma yak e ne?

84. **HANNAH:** Yana lafiya lau, sai dai aiki yayi masa yawa. Kamfanin su sun sami wata babbar kungila, suna ta aiki.

85. **KANDE:** Alhamdillah, abun nema ne ai, ko ko?**(DRINKS)** Yauwa, kin tuna da Tina, yar wajen Yohanna dan uwa na? kusan ma sa'ar ki che

**86. HANNAH:** Tina? Wanda take nazarin ilimin zaman injiniya a foli? Kin hada mu a kauye, ko?

**87. KANDE:** Mahaifinta, ya buga min waya, wai tana son yi "ITin" ta anan kaduna. Na ce ta zauna a dakin ki na da.

**88. HANNAH:** Ba laifi ai, ina take yin "ITin?"

**89. KANDE:** Ba ta samu ba tukunna, ko a tambaye Danjuma ko tana iya yi a ofisshin su?

**90. HANNAH:** **(UNCERTAIN)** Mama, bani da tabbas hakan zai yi daidai, ba mu ma san ta ba ai,

**91. KANDE:** Ni da mahaifinta mun taso tare a gida daya, yar uwa ta ce ita ma ai, kuma tillas ne mu taimakawa juna

**92. HANNAH:** Toh, zan tautauna da Danjuma muji .

**93. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**EPISODE 2, SCENE 4**

**94. SFX:** **FOOTSTEPS COMING ON MIC. BAG DROPPED**

**95. LARABA:** **(CALLS OUT)** Akwai mutun a gidan kuwa? Hajiya Lantana?**(MUTTERS UNDER BREATH)** Ina mutanen gidan?

**96. LANTANA:** **(CALLS BACK OFF MIC)** Laraba? Ina nan a baya fa. Ina zuwa ….**COMING ON MIC)** Maraba, kin jima yau fa.

**97. LARABA:** **(ON MIC)** Na je helkwata saboda in ga darikta.

**98. LANTANA:** Haba? Akwai abinci a kicin, ki je ke diba.

99. **LARABA:** Bana jin yunwa yanzu, na gode hajiya Lantana.

100.**LANTANA:** **(SCOLDS)** Haka, ba zai taimake ki ba fa, eh Laraba, dubi yadda kika rame, kina jin rashin cin abinci zai dawo da Jallo ne.

101.**LARABA:** Ina lafiya Hajiya, bana jin yunwa ne dai kawai, ina yaran?

102.**LANTANA:** Sun je Islamiya, sun kuisan tashi ma, amma ai muna magana akan ki ne ai ba maganan yaran ba.

103.**LARABA:** **(LAUGHS)** Kai Hajiya. Ai ba wani abin Magana akai

104.**SFX:** **<u>RAM BLEETING IN THE BACKGROUND, NIGHT SOUNDS</u>**

105.**LANTANA:** **(SIGHS)** Ya ta. Abin takaice ne kwarai ya same ki, babu wanda zai ga laifin ki idan kin dauke hutu daga wurin aikin ki. Ma'aikatar ma zasu gane ai.

106.**LARABA:** Hajiya, na ma bar aikin.

107.**LANTANA:** **(SURPRISED)** Kai? Haba? Ai ya ma chanchanta ki huta a gida na yan lokaci

108.**LARABA:** Amma fa, na nema a chanja ni ne daga Zaria zuwa wani garin

109.**LANTANA:** **(UPSET)** Wai? Yaushe kika yanke shawarar yin hakan? Me zai sa ki yi nisa da gida yanzu, cikin irin wannan halin? Wannan, ba daidai bane fa, Laraba.

**110.LARABA:** Don Allah Hajiya, tilas kiyi kokari ki gani, na dauwannan shawarar ne domin kare mutunci na.

**111.LANTANA:** Me kike nufi?

**112.LARABA:** Duk maganganun, gunagunin da zage zagen duk inda da shiga …

**113.LANTANA:** **(INTERRUPTS)** Amma, a tsaba fadar maganganu akan ki tun da hatsarin gobarar wutar ta auku ai, basu san abinda suke fad aba ai.

**114.LARABA:** **(HEATED)** Idan maganganu ne kawai da sauki, amma, ki je wasu matan bas u son in duba su wai kada in shafa masu bakin jinni na, a gaskiya, ya ishe ni.

**115.LANTANA:** **(ANGRY)** Wani irin shirimai ne! wato kin riga da kin dage kenan?

**116.LARABA:** **(RESIGNED)** Na je in karbi takarda chanji na yau, bari in ji inda ba ʻa san ni ba

**117.LANTANA:** **(SIGHS)** Za a chanja ki zuwa ina?

**118.LARABA:** Kaduna.

**119.LANTANA:** Kaduna? Ina za ki zauna a kadunar? Ba ki da kauwaye a chan, ba ki yi saurin yin kauwayi ba. Yaya za ki yi Laraba?

**120.LARABA:** Kada ki damu, Hajiya, komai zai daidaita, ina ma da kawaye. Gama Hannah da Maigidan ta Danjuma. Kuma ai, aiki bai zai barni ba balantana inji kewa.

**121.LANTANA:** **(UNCONVINCED)** Toh, kada dai ki maida hankali wajen aiki, ya zaman toh baki da lokacin soyayya da aure.

**122.LARABA:** **(UPSET)** Haba Hajiya! Ya za ki yi maganar wani auren yanzu, bayan Jallon a kwanchi a cikin kabari **.**

**123.LANTANA:** Yi hakuri, ban so in tuna mi ki da zafen mutuwar Jallo ba **(PAUSES)**Amma Laraba, kin tabbata da wannan shawarar.

**124.LARABA:** Hajiya, zan tafi sati mai zuwa, na riga na shiri komai komai

125. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**